
# ABUBUWAN DA YA KAMATA KA SANI GAME DA KACIYAR MATA




**http://fgm.co.nz/where-is-fgm-practiced/**

## Shimfida

- Kimanin mata da 'yan mata miliyan 200 a duk fadin duniya ke fama da munanan illolin yiwa mata kaciya, wadda kuma ake kira da Yanke Matuncin Mata ko Kaciyar Mata, kuma wannan al'ada ta fi yaduwa a nahiyoyin Asiya, Gabas ta Tsakiya da Afrika. (www.who.int/mediacentre/factsheets/fs241)
- Canada ta haramta Kaciyar Mata – Gagarumin cin zarafi ne da za a hukunta masu aikata shi

### Bincike

- ***Uzima Women Relief Group International*** **(Kungiyar Tallafawa Mata ta Duniya *Uzima*)** ta gudanar da wani bincike kan abubuwan da ke damun matan Afrika da al'adar Kaciyar Mata ta shafa, dangane da lafiyar su
- An gudanar da binciken ne tsakanin matan Afrika da ke zaune a Toronto wadanda suka fito daga kasashen Afrika da ake yin Kaciyar Mata a cikinsu
- Maskasudin binciken shi ne gano irin matsalolin kiwon lafiya da matan da aka yi wa Kaciyar Mata ke fama da su da kuma tantance fahimtar su game da dokokin kasar Canada da suka haramta Kaciyar Mata.
- Baicin tattaunawa da matan, an kuma jira'ayoyin al'ummominsu da ma cibiyoyin samar da kiwon lafiya

## Sakamakon Binciken

- An tattauna da mata 21, cibiyoyin lafiya 11 da kuma shugabannin al'umma 8.

- 47% (10/21) na matan da aka tattauna da su, sun ce Kaciyar Matu batu ne da ake kyamar sa, a don haka wasu matan za su ji tsoron bayyana shi ga cibiyoyin kula da lafiyar su
- Fiye da 90% (20/21) na matan da aka tattauna da su, sun fuskanci wani nau'i na Kaciyar Mata da aka yi musu tsakanin lokacin da suke jarirai da kuma lokacin da suka girma. Wannan na nuna cewa mata da dama daga Afrika na fama da Kaciyar Mata
- Dukkan matan sun bayyana damuwa game da cutarwar da ke tattare da kaciyar mata, suna masu cewa raunin da aka ji musu na din-din-din ne ba za a iya kawar da shi ba
- Wasu shugabannin al'ummar sun ce ana Kaciyar Matan ne saboda dalilai na al'ada da addini
- Wasu daga cikin shugabannin addini sun ce za a iya yin tarbiyya ta hanyar ilimantarwa da nusarwa ba tare da an yi wa mutane rauni a jikinsu ba
- Dukkan wadanda aka gudanar da binciken a kansu sun amince cewa Kaciyar Mata na kunshe da mummunan cutarwa sannan suka bayyana damuwarsu game da lafiyar mata da ma al'ummomin baki daya
- Dukkan matan da aka yi wa tambayoyi sun bayyana cewa an gudanar da Kaciyar Matan ne a gida maimakon a asibiti.
- Dalilan da aka bayar na yin Kaciyar Mata sun hadar da:
    - Gusawa daga yarinya zuwa cikakkiyar mace
    - Rage sha'awar saduwa
    - Tanade-tanaden Al'ada/Addini na kare yara mata don tabbatar da cikakkiyar tarbiya da ake bukata a aure
    - Zabin iyali

***Damuwar Al'umma:***

- Tattauna batun Kaciyar Mata da wadanda ba 'yan kabila ba
- Abin kunya
- Abu ne mai wuya a yi neman aure da wadanda ba 'yan kabila ba saboda muzantawar da ke tattare da kaciyar mata a Canada
- Muzantawa irin ta mua'amulla
- Lalata a waje da maza masu aure ke yi
- Sakin Aure

***Damuwar Kiwon Lafiya:***

- Dukkan matan sun yi fama da illolin Kaciyar Mata wadanda suka hadar da:
    - Mummunar damuwa da ke haifar da cutukan tabin hankali kamar su gajiya da ciwon bakin ciki

    - Matsala a mahaifa ko mafitsara
    - Zubar jini mai yawa
    - Kaduwa
    - Wahala wajen haihuwa
    - Raguwar gamsuwa a lokacin saduwa
    - Ciwo a lokacin jinin al'ada

***Damuwar cibiyoyin lafiya:***

- Wahala wajen mu'amala da likitoci
- Cibiyoyin samar da kiwon lafiya ba su da masaniya kan kaciyar mata
- Rashin fahimtar kaciyar mata don daukar matakin yaki da al'adar
- Rashin gamsuwa da cibiyoyin samar da kiwon lafiya saboda:
    - Tsawon lokacin jira
    - Likitoci ba sa bayar da kulawar da ta kamata

## Shawarwarin *Uzima Relief Group International* (Kungiyar Tallafawa ta Duniya Uzima)

- Akwai bukatar ilimantarwa da wayar da kai kan kaciyar mata ga al'ummomi da cibiyoyin samar da kiwon lafiya
- Ya kamata a dauki matakan gaggawa don aiwatar da dokokin da suka hana Kaciyar Mata
- A dauki matakan hana zalunci kai tsaye don karfafa wa mata
- Ya kamata cibiyoyin samar da kiwon lafiya su samar da wasu bayanan hotuna da alamu don nuna goyon baya ga hakkokin mata dangane da Kaciyar Mata
- Ya kamata a samar da tsarin tallafi na al'umma ga mata 'yan asalin Afrika don saukaka mu'amulla tsakaninsu don su tattauna batutuwan al'ada

An samu kudaden gudanar da wannan bincike ne daga

http://www.womensresearch.ca/ www.uzimawomeninternational.org

Karanta cikakken rahoton a shafukan intanet na WCH da UZIMA